# Tsiya Adon'Yan Tauri: Nazarin Ayukkan Kungiyoyin Banga Ga Tsaron Kasa A Wasu Sassan Adabin Hausa

AbdulbasirAhmad Atuwo

**Tsakure**

Tauri lamari ne da ya kasance abu mai matsayi a ƙasar Hausa musamman ta la'akari da irin faɗi-tashin da suke yi wajenƙoƙarin tabbatar da tsaro ga al'umarsu da kuma taimako na samar wa jama'a da magungunan gargajiya da suka shafi cututtuka da kuma na kariyar kai kamar su kas-kaifi da sagau da ba-sanyi da ba-duhu da sauransu ba don komai ba sai domin tsare kansu da kuma al'umma daga ba-zata tare da son nuna jaruntaka da shirin ko-ta -kwana ta hanyar kare al'ummarsu ƙasa baki ɗaya ta hanyoyi daban-daban da suke iyawa. 'Yan tauri da mawaƙansu na da kalmomi da dama waɗanda suke amfani da su wajen kambama kansu a wuraren farauta da bukukuwa irin nasu domin samun damar gwada magungunansu ko makamansu ko nuna buwayarsu da jaruntakarsu. Wannan muƙala ta dubi yadda wasu sassan adabin Hausa suka nuna muhimmancin samun ƙungiyoyin sa - kai na tsaron al'umma ko ƙasakamarƙungiyoyin Banga ko Tauri.daga cikin waɗannan hanyoyi tare da nazarin irin yadda mawaƙansu ke amfani da zaɓaɓɓun kalmomi na tunzurawa domin kambama su domin su yi kwaɗayin ba da ta su gudummawa wajen tabbatar da tsaro a cikin jama'arsu da kuma ƙasarsu baki ɗaya.Haka kuma muƙalar ta dubi littafin "Idon Matambayi" na Muhammadu Gwarzo da "Shaihu Umar" na Abubakar Tafawa Ɓalewa domin ganin irin yadda Marubuta suka fito da nason ƙungiyoyin sa – kai na Banga domin kiyaye tsaron jama'ar ƙasa daga 'yan ta'adda. Wannan shi ya sa aka ba muƙalarsuna " Tsiya Adon 'Yan Tauri: NazarinAyukkan Kungiyoyin Banga Ga Ayukkan Tsaron Kasa A Wasu sassan Adabin Hausa.

## 1.0 Gabatarwa

Lamarin tauri a ƙasar Hausa abu ne da ya samu karɓuwa daɗaɗɗen lokaci da ya gabata, wannan karɓuwa kuwa na da alaƙa ne da irin matsayi na rawar da suke takawa wajen tunkarar abokan gaba ba tare da tsoro ko shakka ba da ƙundumbala a yanayi na ƙunarbaƙin wake wanda sai tsayayyun jarumai marasa tsoro ko karayar zuci ke iya yin haka.Haka kuma a sana'o'i masu wuya kamar farauta duka fannoni ne da ke buƙatar tsayayyun mazaje waɗanda ba su da alamar tsoro.

Kasar Hausa ta yi fama da yaƙe-yaƙen cikin gida har ma da na wajen, Daulolin ƙasar Hausa ƙarƙashin Sarakuna sun yi ta famar gwagwarmayar yaƙe-yaƙen kariyarkai har ma da na faɗaɗa mulkin garuruwa da ƙasashe. Ashe al'ummar da ta fito a wannan yanayi ba a mamaki a samu jama'ar 'yan tauri a cikinsu.Kafin a shiga aiki gadan-gadan akwai bukatar a taɓi muhimman kalmomi da ke cikin taken muƙalar.

## 2.0 Asalin KalmarTauri

Asalin kalmar "Tauri" na da alaƙa ta kai tsaye da manufar in maganin taurin ya yi tasiri wato yadda jikin mutum kan koma bayan cin maganin.Wato jikin mutum zai yi tauri yadda ba ƙarfen da zai fasa jikin mutum komai kaifinsa komai tsininsa da nauyinsa.Kamaryadda Bunza, (1999) ya bayyana asalin kalmmar Tauri da cewa:

> "Kalmar tauri daga "Tauri" take mai nufin abu ya ƙifasawa ko ya ƙi barin a sarafashi yadda ake so, komutumin da ya faye ƙin karɓar shawara, akan ce wane tauri kegare shi. Mai irin wannan sirin na maganin ƙarfe irin wuƙa, da takobi, da mashi da duk wani makami na ƙarfe ba su fasajikinsu. Haka kuma yana iya sarraffa ƙarfe yadda yake so ba tare da wata wahala ba."

Wannan ɗabi'a ta sarrafa ƙarfe ba tare da ya aibanta ko cutarwa ba shi ya sa ake cewa tauri masu tu'ammali da wannan harkar kuma ake kiransu 'yan tauri.

## 2.1 Ma'anar Tauri

An samu ra'ayoyin jama'a kan ma'anar tauri. Kamusun Hausa (2006:433) Ya bayyana tauri da cewa "shi ne maganin da aka ci domin kashe kaifin wuƙa ko wani makami don ya kasa huda jikin mutum". Bargery,(1934:1009) ya bayyana Tauri da "Tsananin kaifi". Bunza,(1990)ya bayyana tauri da cewa "Magani ne da ya samo asali daga taurin jiki. Watau mai irin maganin, jikinsa zai yi wa ƙarfe tauri, ba ya fasa shi."Abin lura a nan shi ne, samun wani magani na ci ko na sha ko na shafawa ko na laƙawa wanda zai sa jiki ya yi tauri ba ya fasuwa ga wuƙa ko mashi ko makamantansu shi ne tauri. Kuma waɗanda ke cikin wannan harka ta tauri su ne ake kira 'yan tauri. A waƙar Kassu ta Bala Naladi yana bayyana mana ma'anar tauri da cewa:

Bai dai raba gora da goro ba,

In dwan ƙarhe alewa na,

Shi shi ka samu shi mirgiɗe.

Kassu Zurmi,Waƙar Bala na Ladi

Wannan ɗan waƙa na nuna abin da ake nufi da tauria taƙaice. Domin anbayyana Bala Naladi a matsayinsa ɗaya daga cikin sanannun 'yan tauri, ga shi wasu siffofi da ke nuna shahararsa a tauri. Wato mayar da gora tamkar goro; sannan yana sarrafa duk wani makamin ƙarfe tamkar yadda ake sarafas alewa.

## 2.2 Tsiya Da Fatara A Matsayin YaboGa'Yan tauri

Tsiya ko fatara ko rashi ko talauci duka abubuwa ne ɗaya ko makusantan juna da ke tare da rayuwar mutum, sai dai babu jinsi na jama'a ko ƙabila ko addini da ya yi aminta da a alaƙanta shi da tsiya sai 'yantauri. Bisa ga al'ada ana iya cewa tsiya da tauri tamkar aminan juna ne a rayuwar 'yan tauri.

Yayin da ake danganta wanda ba ɗan tauri ba da tsiya ya ji an ci zarafinsa ko an wulaƙanta shi ko ka tozarta shi, idan ɗan tauri ne zai ji an daranjanta shi an ɗaukaka shi an mutunta shi har ya kai ga tsima yana kyarma yana kirari. Sai dai wannan muƙala ta kasa tsiyar tauri zuwa gida biyu: kuma ana iya fahimtar wannan rabo a bayyane cikin waƙoƙin makaɗansu da kambawar da suke yi wa 'yan tauri

1. Tsiya mai nuni ga ma'ana ta asali, wato fatara ko rashi
2. Tsiya mai nuni ga rashin tsoro da naƙaltar faɗace-faɗace ko tankiya ko tashin-tashina

### 2.3 Tsiya Ta Fatara

'Yan tauri na fahari da tsiya da fatara da rashi, domin basu ra'ayin a danganta su da duk wata harka ta arziki ko jin daɗi a rayuwarsu ta duniya.Muna iya ganin wannan a waƙoƙi da kirarin 'yan tauri daban-daban musamman waƙoƙin Kassu Zurmi da na Garba Ɗanwasa. Misali a waƙar Garba Ɗanwasa ta'Ɗan Musa Ɗantaragon yana cewa:

Jagora: Jama'a kun ga Ɗantaragon Fatara

Kun ga Ɗan taragon tciya

Ga Ɗantaragon tciya.

Garba Ɗan wasa, Waƙar Ɗan Musa Ɗan tarago

Kalmar 'tarago' a ƙamusun Hausa,(2006:428) da ƙamusun Bargery,(1934:996) duk sun nuna cewa "Mazaunin fasinjan jirgin ƙasa mai kama da ɗaki." A nan Ɗan wasa ya yi amfani da jinsantarwar da ake wa Ɗan tarago a matsayinsa na mutun zuwa taragon fatara da tsiya. A waƙar Kassu Zurmi ta Nomau Namagarya yana cewa:

Jagora : Gagarabadau uban gidan 'Yaj jima,

Da Kassu barka da tciya,

Banawa kyawon faɗa ayo accakwama[1],

Baba a shirya ta baƙiƙirin ta ƙare muku can

--------------------------------

Kassu Zurmi, Waƙar Nomau Namagarya

Wannan ɗan waƙa da Kassu Zurmi ya fara da yi wa Nomau jinjina kalmar kinaya ta "gagarabadau" tare da danganta shi da matarsa da kuma makaɗinsa. Sannan shawara ta biyo baya kan yadda ya kamata samari su tunkari kowane irin faɗa wato da salo iri na ƙudumbala da Kassu ya kira "accakwama".

Kalmomin da mawaƙan 'yan tauri ke amfani da su zaɓaɓɓu ne domin zuga tunzurawa gaɗan tauri cikin sauƙi.A irin yanayi fa ɗan tauri ba ya ganin haɗarin duk wata fitina ko tankiya dake fuskantarsa sai ya faɗa. A waƙar Nomau na Magarya ta Kassu Zurmi ya yi amfani da kalmomi kamar su 'Gauɗe'[2] da'Kanƙari'[3] da 'Doƙoƙiso[4]' misali yana cewa:

---

[1]Wannan kalma tana nuni da ƙundumbala ko ƙunar baƙin wake.
[2]Nau'in ice ne mai gautsi
[3]Wani mulmulallen dutse mai wuyar fashewa
[4]Wanda ba ya ja da baya fagen fitina ko faɗa.

Jagora: Gauɗe ba ka matanki,

Baba kaɗe baka baka,

Na Magaji ƙanƙari,

Ko Allahu na ruwa ba ka jiƙa,

Doƙoƙiso ko ba ka jin batun masu gari.

Kassu Zurmi, Waƙar Nomau Namagarya

A cikin wannan ɗan waƙa ta Nomau Na magarya, mawaƙinya haɗa da kalmar salon kinaya kamar: "Doƙoƙiso" da kuma salon "Alamtarwa "kamar: "Gauɗe" kamar " Ƙanƙari" duk waɗannan kalmomi, Kassu ya yi amfani da su ne domin nuna matuƙar fatara da tsiyar Nomau.

Duk waɗannan 'ya'yan waƙar suna nuni da matuƙar tsiya da ke tare da su har ta sa ba su da amfani ga kansu balle jama'a.A waƙar Nomau Namagarya Kassu Zurmi ya yi amfani salon siffantawa kamar a cikin ɗan waƙarinda yake cewa:

Jagora: Nomau Tushen hwaɗa Karen masu gari

Torankawan tsiya uban mai rogo,

Ko hwatara tai yawa takan zan Iko,

Nomau ko ba ka jin batun masu gari.

Kassu Zurmi, Waƙar Nomau Namagarya

A nan kalmar 'Torankawa' sunan wani jinsin al'ummar wasu Fulani ne. Asalin Shehu Usman Ɗanfodiyo daga wannan jama'a ya fito. Irin gwaggwarmayar da Shehu ya yi wajen yaɗa Musulunci a Kasar Hausa ya sa kalmar da jinsin al'ummar sun samu wani matsayi da daraja da har kalmar ta zama wani abin siffantawa ga shaharарsu fagen yaɗa Musulunci ko asuli. A nan shi ne Kassu Zurmi ya yi irin wannan siffantawa, inda ya siffanta Nomau da 'Torankawan tsiya' domin nuna shararsa ga tsiya. Kamar misali idan ana son a ba da misalign Torankawan arziki a ce 'Torankawan arziki Aliko Ɗangote'

A waƙar Zayyanu Ɗanwasa Gummi da Ɗan Musa Ɗantarago ya gadar wa Ɗantarago tsiya ga uwarsa da ubansa kamar haka:

Jagora: Wai Bawa wag gadi tciya ƙasa da sama?

Wag gadi tciya Ɗantarago?

Kun gadi tciya Duna Karo

Ga Ɗan Musa Ɗantarago

NaLema uwayen hitina."

Zayyanu Ɗan wasa, Waƙar Ɗan Musa Ɗan tarago

A wannan ɗan waƙa Zayyanu Ɗan wasa ya nuna irin dangantakar Ɗantarago da tsananin tsiya domin gadon abarsa ya yi. Sannan Zayyanu ya yi amfani da salon kinaya da irin kalmomin 'yan tauri da su ke amfani da su wajen kirari ko yadda mawaƙansu ke kiransu a matsayin sunayensu inda ya kira shi'Duna' wanda ya yi kama da su 'Dogozo' da su 'Ɗan kurjan' 'yan tauri na amfani da su domin razanarwa da firgita abokan gaba kafin a kara.Shi ya sa mawaƙin ya kira shi 'Uwayen fitina'

A waƙar "Karen Ayya Maidubu Kassu Zurrmi ya nuna irin yadda tsiyar ta yi wa Maidubu yaaɗo har ga sana'arsa har ga sana'arsu ta noma inda yake cewa:

Jagora: Ya yi dubu kuma

Ya dubu kuma

Ya yi dubu amma huɗu na ƙyasuwa.

Kassu Zurmi, Waƙar Karen Ayya Maidubu

A kalmomi irin na manoma, idan an ce wa manomi 'Ya yi dubu' to babban yabo ne da abin alfahari a gareshi saboda 'dubun' na nufin na damin dawa na gero ko na maiwa ko kuma buhu dubu na masara ko na shinkafa ko na alkama. To Karen Ayya nasa har dubu huɗu ne, amma saboda alaƙa da tsiya suka ƙyasuwa ne ban a abinci ba.

Ba a nan ba kawai, idan muka koma a waƙar Shayi Ɗangidan Labbo ta Kassu Zurmi a Gusau, (2009) Ya nuna yadda Shayi ya yi da tantabarinsa. Tantabarin dai asalinsu na gado ne aka bar masa amma saboda tsiya duk sun ƙare shi kaɗai ya rage.

Jagora: ------------------------------

Sai in shayaya yaɗ ɗago ɗaki,

'Yan mazan tantabarin ga na yi mai guɗa,

Shi ƙuɗunguru Shayi Ɗangidan Labbo,

Shi ko kokirzon sai ya watsa yat tsaba,

Kai ko tsuntsu tcince tciyakku ta bi ku.

Kassu Zurmi, Waƙar Shayi Ɗan gidan Labbo

A wannan ɗan waƙa, Kassu ya yi amfani da salon jinsartarwainda ya nuna tantabarin Shayi yanayi wa Shayi guɗa ta hanyar zama masa ɗan ma'abba. Mun ga yadda aka yi amfani da salon kinaya inda tantabarin ya kira Shayi dakalmar 'Kudunguru' domin nuna tsiya. Shi ma Kassu ya yi amfani wata kalmar kiniya wato 'Kokirzo' da kuma layin ɗan waƙarda Kassu ya rufe da shi wato 'Kai ko tsuntsu tcince tciyakku ta bi ku'. Wannanya nuna tsabar da aka watsa wa tantabarin ta tsiya ce domin an ce 'tcince'ya nuna tsabar ba ta da yawa, kamata ya tsinta ya bari da akwai wadata.

### 2.3 TsiyarFaɗa Ko Tankiya

'Yantauri sun shahara wajen ƙulla faɗace-faɗace da tashin-tashina.Ɗabi'ar tauri na tattare da tsokana tsakanin ƙungiyoyin adawa na tauri. Sau da yawa sukan asalta farauta a yi gangami gari da gari ko ƙasa da ƙasa domin kawai a je a kece raini da gwaje-gwajen magunguna da makamai a tsakanin juna, Umar, (1987).

Kirari, wata matattara ce ta musanyar zafafan maganganu da kambama juna a dandalin tauri. A cikin waƙar Zayyanu Ɗanwasa Gummi ta Ɗan Ali, ga kirarinsa:

"Kai Zayyanu kai!

Kada in ƙara ji,

Kada in ƙara gani,

Kada in ƙara jin kirarin yaro ɗan tcelen uwa,

Na san yaro ko maganin jini bai sha ba,

Na ce mai sara guda shi hwaɗi shi ribce,

Kullum roƙon Allah ni kai,

Shi koro hwaɗan zube ban ƙwarya,

Mu kai ma likkita aiki,

Ni ko a sa mini inkawa,

A kai ni Kanwuri Ɗan Ali,

Sarki ya ce mini halama ka yi halinka,

Hwaɗa ma masu iko cikin gari suka iko,

Ni ko daji ni ka iko."

Wannan ɗan waƙa ya ƙunshi kambawa da tunzurawa domin kirari ne Ɗan Ali ke yi lokacin da duk aka buga takensa. Idan aka dubi kalaman Ɗan Ali a cikin kirarinsa, ana iya yi musu gida uku: Na farko akwai koɗa kai inda yake cewa'Kada in ƙara jin kirarin yaro ɗan tcelen uwa' ya nuna duk wanda ke nan yaro ne.Sannan akwai al'adarsu ta neman tayar da fitina'Kullum roƙon Allah ni kai,Shi koro hwaɗan zube ban ƙwarya' saboda irin wannan yanayi ne suke gwada ƙarfin jaruntakarsu da ingancin makamansu

Har yanzu idan aka dubi waƙar Garkuwa ta Farautar Dakatsalle wadda ya yi wa Sufeto Nuhu Ɗansanda ta ƙara bayyana yadda 'yan tauri ke danganta kalmar tsiya da tankiya ko hargitsnin faɗa.

-----------------------

Jagora: Wani ƙato ya shigo fili,

Rigarsa dut ta kekkece

Na ce Mabaraci ne

Ga naira goma ku miƙa mai

To ashe mai shibka *tsiya* ne shi

Akwai ƙaho cikin riga

Sai ya zaro ƙahonsa shi

Ke nan ya fara hurawa

……………………..

Ashe nan na faɗa durun 'uwa

Kafin in waiwaya Mamman

Sai ga kan mutum cikin fili

Ya faɗo ƙiri da gemunai

Gangar jiki baya nan

Tabɗi rannan ne na ga durun uwa

Na ga mutum bakwai kwance

An yanke su kamar kaji."

Garkuwa, Waƙar Sufeto Nuhu Ɗan sanda

An kawo wannan ɗan waƙa ne domina bayyana wasu abubuwa guda uku da muƙala ta nuna akan abin da ya faru a wannan farauta ta Dakatsalle na kalmar 'Tsiya' mai dangantaka da tankiya ko faɗa . Kamar yadda ya gabata 'yan tauri kan ɗauki kalmar tsiya ko tsiya ta asali kokuma tsiya ta faɗa ko tankiya ko ta'addanci. A nan idan aka duba abu na farko, ƙaton da shigo fili, siffarsa ta tsiya ce.Har ma Garkuwa ya yi tsammanin almajiri ne ya ba shi sadaka.Abu na biyu, ɗan waƙa ya nuna tsiya ta faɗadomin a ɗan waƙa gashi an nuna: ''To ashe mai shibka *tsiya* ne shi'' abu na uku shirya farauta domin kawai a je a gwada jarunta daga ƙarshe lamari ya ƙare da kashe – kashe kamar yadda ɗan waƙa ya nuna:''Kafin in waiwaya Mamman, Sai ga kan mutum cikin fili''. A wata mai nuni da tsiyar 'yan tauri a faɗa, a waƙarDogozo Duna Kasko ta Garba Ɗanwasa na cewa:

Jagora: Yau Garba kar ka koma kiɗi sai in ta samu,

Tun da kag ga raina ya ɓaci ga dajin ga,

Ban da kunne ban da hure shina Ɗan wasa,

Yau na zo da masu ɗaukar kaya yara,

Da karnai duw wanda nig gani in sare kai nai,

Kafin a jinjima Dogozo ya yo ɓarna.

Garba Ɗan wasa: Waƙar Doozo Duna Kasko

A wannan waƙa, Garba Ɗanwasa ya nuni da wata farauta ta fitina inda aka Dogozo ya zubar da jinin mazaje. A cikin wannan Ɗan waƙa, Ɗan wasa ya yi amfani da salon fira tsakanisa da Dogozo. Tun daga layin farko har zuwa na biyar duk Dogozo ne ke magana sai layin ƙarshe ne Ɗan wasa ya fara bayyana aikin da Dogozo ya yi "Kafin a jinjima Dogozo ya yo ɓarna"

Amshi: In ga mutum ɗari hululu duy ya sassare,

Sa maza gudun daji bawan mai ganga,

Mai barandami mai adda kura zagau,

Ci da ƙarfi mugun bori mai ban tsoro,

Maƙi sake baran Malam wa nah hwaɗa ma?

Ina Amali toron giwa watce farauta?

Mai hwarakke mai mashi ga ice yashe,

In ka ƙi gurgusawa wahala na hwaɗa ma.

Garba Ɗan wasa: Waƙar Doozo Duna Kasko

A wannan ɗan waƙa, Garba Ɗan wasa ya yi amfani da salon kinaya sosai kamar: ''bawan mai ganga'', ko ''Ci da ƙarfi mugun bori'' ko ''Maƙi sake'' ko ''Amali toron giwa'' daga nan sai nuni ga irin kayan da Dogozo ya mallaka da cewa ba na alheri ba ne. Kamar ''Mai hwarakke mai mashi ga ice yashe'' wanda kowanne cikin su mugun makami ne duk wannan domin a nuna tsiya faɗa ta 'yan tauri

Jagora: Nic ce tsaya-tsaya ɓarna ta kai ɓanna,

Yac ce kashin mutum ɗari ba ɓarna ba,

A wa mutum ɗari rotce ba ɓarna ba,

Mai kiɗi kyan hwaɗa a bar kai hannu na can,

Yara masu ɗaukar kaya su taho birni,

A tambaye su manyan daji ba su tanka ba,

Suna kurum suna sumalin babbar ɓarna,

Su ce ma 'yan uwa su zo da gado daji ya motsu,

Don ba bu lahiya manya na can kwance,

Suna cikin kalage ba mai ko motci.

Garba Ɗan wasa: Waƙar Doozo Duna Kasko

A cikin wannan ɗan waƙa, Ɗanwasa ya fara mayar da jawabi a hirarsu da Dogozo. Kuma yana bayyana irin ɗabi'ar Dogozo wadda ya sani ta haddasa tankiya dakuma aikata tsiya mai yawa irin tasu. Abubuwan lura a cikin wannan ɗan waƙa. Da farko dai ɗan waƙar na cike da kalmomin ta'addanci kamar:"ɓarna ta kai ɓanna" da "kashin mutum ɗari ba ɓarna ba" ko"Su ce ma 'yan uwa su zo da gado daji ya motsu" a nan tafiya na da gado nufin a ɗauko gawawwakkin da Dogozo ya kakkashe. Na biyu wannan farauta da Dogozo ya yi wannan ɓarna ta yi kama da wadda ta auku a farautar Dajin Rayya da Kassu ya yi labarta a cikin Shaho. Wannan ya nuna cewar a duk lokacin da 'yan tauri suka ƙulla farauta to takan ƙare da tsiya ta faɗa. Haka wani abin lura wajen faɗan 'yan tauri shi ne, kowace ƙungiya ta san irin salon saran da 'yan ƙungiyarsu ke ta ke yi. Misali, Kassu na cewa:

Jagora: "Kotsayin wata, ko shan doguwa"

Kun san shan doguwa 'yan yara?

Tsayin adda, hannu ya birke bai aiki,

Tsayin wata kau saran adda irin na Nagunda,

Su nah hwalkace mi goshi,

Rijiya ga baya kau,

Saran nan na Annen Dayan,

'Yan Jabanda na sare,

Su nah hwalkace mai allo,

………………………..

Aikau kwance, Sani kwance,

Suri kwance, Kogo kwance,

Inga nig ga sun halbe shi

Na san waɗa Kaurad dawa nan wani,

Yas shekara bai yi ko kunya ba.

Kassu Zurmi: Waƙar 'Yan Janbanda

Wannan ɗan waƙa na ƙunshe da wata tsiyar duk da yake ba fagen farauta ba ne, tamkar tankiya ce da 'Yan jabanda suka shirya da nufin ɗaukar fansa ko tsige raini daga take-taken da abokan adawa suke yi musu. Haka kuma tsiyar ta haddasa zubar da jini da nakasa sassan jikin manyan 'yan tauri. Kassu bayyana nauo'in sara ko raunin da suke wa juna wajen tsiyarsu ta tankiya, Misali: "Ko tsayin wata, ko shan doguwa" watohannu ya birke bai aiki, "Tsayin wata kau saran adda irin na Nagunda, Su nah hwalkace mi goshi" ga wani nau'in sara kuma inji Kassu "Rijiya ga baya kau,Saran nan na Annen Dayan,'Yan Jabanda na sare,Su nah hwalkace mai allo". Wani abu na uku da ɗan waƙar ya ƙunsa shi ne manyan 'yan tauri da tankiyar ta rutsa da su kamar haka: "Aikau kwance, Sani kwance,Suri kwance, Kogo kwance,Inga nig ga sun halbe shi". A layukan ƙarshe na ɗan waƙar Kassu ya nuna mutum na biyar ne cikin waɗanda aka jikkata, wanda ya shekara bai yi noma saboda jinyar harbin bindiga da aka yi masa.

Sai dai duk waɗannan matsalolin da 'yan tauri kan faɗa na sunan faɗace-faɗace, ba su ɗauke su ɗauke su komai ba face jaruntakam da cika da kamala irin tauri. Saboda haka shirye suke su tunkari kowace irin tankiya ta taso ko ga al'ummarsu ko ga 'yan uwansu ko a kansu kuma ga ƙasa baki ɗaya.

### 3.0 Kalmar Banga /'Yan banga Da Ma'anarta

Kalmar "Banga" sunan wata 'yar ƙaramar ganga ce da ake amfani da ita wajen yin kiɗan jaruntaka ga sarakuna musamman wajen yaƙi. Kamusun Hausa (2006:35) ya nuna cewa 'Banga' wata ƙaramar ganga mai kama da kuntukuru mai faɗin baki da tsukakken baya wadda galibi akan kaɗawa sarakuna ita. Sannan Kamusun ya ƙara bada wata ma'ana da cewa "Banga" it ace ' kariyar 'yan tauri ke yi wa shugabannin siyasa. An fi saninsu da suna 'yanbangar siyasa.Haka kuma kalmar 'Banga' na nufin wata nau'in 'yar riga mai kama da riga 'yar 'shara' ko 'binjima' ta Fulani, ana yinta da kaloli iri – iri a ƙasar 'yan tauri a da har ma a yau a wasu wurairai suna amfani da irin wannan rigar.

Anan idan aka duba, kalmar 'yan 'banga' ana alaƙanta ta da duk waɗannan bayanai. Misali : Banga na bayanin sunan ganga, ana kiransu 'yan banga domin yadda ake kaɗawa sarki itawajen yaƙi domin kambama shi sannan ya tunzura'yan taurinsa, su kuma su tsima su fara kirari domin nunawa sarki irin jarumawanda ke tare da shi a fagen fama.

Sannan nau'in rigar da ake kira 'Banga', ana kiran su 'yan banga ne saboda irin nau'in rigar da suke sanye da itane a koyaushe mai kaloli iri-iri musamman tsanwa da rawaya da bulu da ja. Ko ina ka gansu ka san 'yan tauri ne ko 'yan banga masu jiran ko ta kwana.

Wannan kalma ta 'yan banga ayukkanta sun dade, ana iya cewa ayukkanta sun fara tun lokacinda Bahaushe ya fara fuskantar barazanar hare-hare da yake-yake da ƙalubalen miyagun halaye na fashi da makami da sace-sace da sane da sauran dabi'u na tashin-tashina da ke addabar al'umma tun a lokacin har bisa yau waɗannan matsaloli sun tilasta wa al'ummar Hausawa har ma da maƙwabtansu kafa ƙungiyoyi da zasu sadaukar da kansu wajen kariyar lafiyarsu da dukiyoyinsu. Bayyanar matsaloli irin na rashin tsaro na daga cikin dalilin da suka sa 'yan tauri su riƙa haɗuwa domin tunkarar barazanar waɗannan matsaloli na ta'addanci.

### 4.0 'Yantauri Da Kungiyar Banga A Aikin Tsaron Al'ummar Nijeriya

Ganin yadda ungiyar Boko Haram ta addabi Nijeriya da sauran nau 'o'in barazana da faɗace-faɗace tsakanin makiyaya da manoma da tsagerancin tsagerun Niger Delta da yawaitar garkuwa da mutane da tarzomar addini da kabilanci da yawaitar kisan gilla da kisan siyasa da kisan ayukkan matsafa . Matsin waɗannan matsaloli ya sa rashin tsaro ya ƙara faɗaɗa kenan bukatar tsaro ta yawaita. Har yasa anfara kira ga gwamnati tun lokacin shekara ta 1999 wato gwamnatin Olusegun Obasanjo, sai dai wannan batu bai samu kulawar gwamnatin tarayya ba sai lokacin shugaban ƙasa maragayi Umar Musa 'Yar 'adu'a wanda shi ne shugaban ƙasa na farko da ya fara na'am da karɓuwar 'Yan banga a hukumance ranar 27 ga watan Afrilu, 2004, da sunan Kungiyar 'Yan banga ta Nijeriya, wato vigilante group of Nijeriya (VGN)a matsayin wata ƙungiya mai tallafawa sauran sassan tsaro na Nijeriya.

Wannan batu na 'Yan banga ya samu matsayi da karɓuwa a wasu jihohi, sai dai ta fuskoki daban daban har uku . Wasu sun daukeshi ta fuskar 'Yan sandar Al 'umma "community police" misali, jihar Sakkwato, gwamnatin jihar a wannan lokaci Aliyu Magatakarda Wamakko,Sakin Ymman Sakkwato yakira nasa "Sokoto State Security corps" su kuma jama'a suna kiransu 'Yan sandar Alu.

Fitowa da wannan al'ummar ta tallafa wajen wannan tsaro a Jihar Sakkwato da dama musamman wajen samarwa matasa aikin yi wanda ya rage ambaliyar tsageron yara da sace-sace da kashe-kashe da sauran yawaitar ayukka masu nasaba da rashin aikin yi da matasa. Sannan su kansu 'Yan sandar Alu suna taka rawa wajen daidaita tsaro da tabbatar da bin doka da oda a tsakanin al'ummarsu.A Kano, Hisba ce hukumar da ke wannan aikin.Su'Yan kareta doka odarta shafi ababen hawa ne aikinsu.

A Jihar Oyo, inda aka ɗauki su kimanin 11,000 inda ake kiransu da sunansu wato V.G.N. Kungiyar 'Yanbanga ta Nigeria. Kuma al'ummar yankin suna nuna gamsuwarsu ga yadda suke sadaukar da kansu wajen tabbatar tsaron lafiyarsu da dukiyoyinsu (Freedom Online).

Idan muka dubi yankunan da ta'asar ayukkan Boko Haram suka yi katutu,Kamar Maiduuri da Yobe da Adamawa, tsananin rashin tsaron yake da yawa ana kiran 'Yan bangar '' Haɗakar Jami'an tsaro na farin kaya (Civilian J.T.F)[5] wannan haɗakar ta haɗa dukkan nau'o'in jami'an tsaro masu kaki da 'yan banga masu ayukkan sa kai na yankin. Wannan haɗakar ta yi matuƙar tasiri wajen yaƙi da 'Yan Boko Haram. Musamman ganin cewa 'yan Bangar su ne 'yan gida kuma su ne suka san wane ne ba wane ne ba a ciki da wajen harkar Boko Haram da sauran ayukkan assha da ake aikatawa a yankin.

A yankunan ƙasashen Igbo da makusantansu suna da irin waɗannan ƙungiyoyin na 'yan Banga. Sun gudana tun kafin zuwan Turawan yamma a yankunan al'ummomi Igbo, Okeke, (2013:311)[6] akwai ƙungiyoyin maskured waɗanda manufarsu shi ne tabbatar da tsaro, sannan daga bisani ƙungiyoyi irin na unguwanni duk asalinsu na 'yan banga ne sai dai daga baya masu jagorantarsu su karkatar da manufofinsu na asali zuwa son rai.

---

[5] J.T.F .(Joint. Task Force) wato haɗakar aiki da cikawa ta jami'an tsaro da 'yan Banga.

[6] Okeke V.O.S.(2013: Community Policing, Vigilante Security Apparatus and Security Challenge in Nigeria: A lesson from Britain and Igbo traditional Security in Nigeriya"

**5.0 Nason Kuniyoyin Banga Da Na Sa – Kai Da Aiyukkansu A Wasu Litattafan Zube Na Hausa**

Irin yadda lamarin nason tanadin tsaro ya ginu a tunanin Bahaushe,ya sa ana ganin tasirin wannan nason ƙarara a wasu harkokin rayuwa na ƙasar Hausa kamar yadda wasu biranen ƙasar Hausa suke zagaye da gine – ginen ganuwa da sarautu masu nasaba tsaro kamar sarkin yaƙi ko magayaƙi ko lihidda ko muƙamai masu alaƙa da jagorancin ƙungiyoyin sa – kai kamar sarkin karma wato shugaban 'yan tauri da shugaban 'yan banga da makamantansu. Kamar yadda in nason tsaron ya bayyana waƙoƙin baka da kirari musamman na 'yan tauri kamar a bayanan da suka gabata, haka ne nason ya shafi rubuce – rubucen Bahaushe nalabarun zube. Wannan ɓangare na wannan muƙala ya dubi nason ƙungiyoyin tsaro wasu labarun zube.

A littafin Gwarzo, (1934)mun ga irin yadda ƙungiyar ɓarayi ta Idon matambayi da jama'arsa suka dami jama'a da sata da kashe – kashe. Wannan ya tilasta wa jama'ar kafa ƙungiyar 'yan gadi wato makamanciyar ƙungiyar 'yan banga kuma suka yi ta famar yaƙi da su da gungun ɓarayin. Misali:

> "Yana ta ja da baya suna bin sa, har ya sami dama ya zaro wuƙa daga kube. Ya riƙe ta a hannunsa. Sai Sarkin gadi ya yi kusa da shi zai kama shi. Idon matambayi ya soke shi da wuƙa a ƙahon zuci. Sai Sani ya faɗi matacce. Sauran 'yan gadi kuma suka ta gudu".[7]

A cikin wannan bayani muna iya fahimtar ƙoƙarin da jama'asuka yi tabbatar da ƙugiya ko ta 'yan banga ko mai kama da ita domin tattalin tsaron kansu da dukiyoyinsu, saboda ga ɓarayi ko 'yan fashi suna ba-ta-kashi da jama'a har da kisan kai. Sannan muna iya fahimtar har shugaba garesu mai suna Sani a matsayin sarki ko shugaba.Haka ga wani bayani makamancin wannan mai nuni ga lamarin ayyukan banga:

> "Ɗangadi ya kai wa Idon Matambayi duka da sanda ya same shi.
>
> Idon Matambayi ya yi fushi ya yi maza ya zare takobi ya fille kan
>
> Ɗangadi ya faɗi matacce".[8]

Wannan bayani na nuni da irin yadda Ɗangadi ya nuna ɗabi'a irin ta 'yan tauri ta rashin shakku ko tsoro ga tunkarar sababi komai gimansa. Kuma da ƙarshe ɓarawon ya zama ajalinsa.Idan muka shiga littafin Tafawa Ɓalewa, (1934:20)*Shaihu Umar*daidai indaƊansane ya sace Umar ya shiga da shi kogon dutse a wani sunƙurun daji. Daga bisani wasu jama'a 'yan sa-ka sun fantsama cikin daji harinda yake ɓoye daUmar kuma ga abin da yake cewa:

> Da masu nema na suka kusato kogon inda muke, sai wani daga cikinsu ya ce,

[7]Gwarzo, (1934: 20)

[8] Gwarzo, (134: .30)

"Kada mu wuce wannan wuri, domin da na sani a wajajen nan akwai wani kogo

Inda wata rana da muka fito gudummuwa muka kama wani ɗan sane da ya sato

yarinya. Sai mu je mu duba nan tukuna, in ba bu komai mu wuce" Duk abin da

suke faɗi muna ji. Sai mutumin nan ya ɗauko wuƙa tasa ya aza mini a wuya , ya

ce in na yi magana ko ɗan motsi ma lalle zai yanka ni"

Idan aka dubi bayanin da sama sai lura da abubuwa biyu da suka danganci wannan muƙala, da farko dai wannan mutum Umar ya ji yana magana yana daga cikin 'yan sa-kai domin nemo Umar da tabbatar da tsaronsa. Sannan abu na biyu, bayin wannan mutum ya nuna cewa wannan sane ba shi ne na farko ba an taɓa sace wata yarinya wani lokaci a baya, kuma a wannan kogon suka kama ɗan sanen tare da yarinyar

Muƙala ta lalubo wani misali daga littafin Imam, (1937:22-25) wato *Magana Jari Ce 1* a labari mai taken" Banza Ta Kori Wofi". Labarin ya nuna yadda 'yan gadi suka tunkaari wasu ɓarayin rogo saidai da ya ke ƙauyawa ne kuma sabon-shiga, sun kasa kama ɓarayin, kamar yadda wani bafade ke wa sarki bayanin abin da ya faru kamar haka:

"Waɗannan 'Yan Gadin waɗansu sakarkarun ƙauyawa ne, sabon shiga.

Da jin yadda suka tasam maɓarayin nan da hauka haka, a ka san gaulaye

ne, tashin ƙauye ka san 'Yan Gadin ne na sosai, Allah ya ba ka nasara, sai

su laɓaɓa da yake a na duhu, su kama su a hannu ba su sani ba; to ka ga

yadda suka ɓata al'amarin."

A wannan bayani muna iya ganin nason aiyukkan 'yan banga a cikin labarin.

**5.0 Kammalawa**

Tauri a ƙasar Hausa, lamari ne da ke tattare da abubuwan da ke buƙatar a yi nazarinsu, sannan a yi tunanin inganta su yadda zasu ƙara zama masu amfani ga al'umma maimakon ayukkan tankiya. Misali a dubi al'adun 'yan tauri na jaruntaka da rashin tsoro da tsura da tsoratarwa da ya zama wani ma'auni na iya tunkarar duk wata tankiya ko tashi-tashina yadda watakila hukumomi da ƙungiyoyi masu zaman kansu ko jama'a masu abun hannunsu sun ɗauki nauyin yi musu wani horo a kan wani yardadden tsari yadda za su taimaka wa ƙasa baki ɗaya ta fagen kariya da tsaro, maimakon faɗa da barazana ga junansu.

Ganin irin yadda tsaro ya takaita a Nijeriya, al'ummar ƙasar sun yi na'am da kafuwar Kungiyar Banga ta Kasa kamar yadda ɗaya daga cikin uwayen ƙungiyar ta kasa Oba Lamidi Olayiwola Adeyemi ya yi bayani, ya ce irin yadda ta'addancin ke yawaita a cikin al'umma ƙarfafa irin waɗannan ƙungiyoyi ya zama tilas. Sannan jama'a sun yi na'am da ayukkan Kungiyar 'Yan Banga. Sannan idan anyi la'akari da maganar Babban Kwamandan Kungiyar ta kasa Mista Sunday Olajide da yace duk da yake ma'aikatan 'yan banga ta ƙasa suna aiki ne akan kishin ƙasa ba mai karɓar ko sisi a matsayin

albashin aikinsu, kuma yawansu ya kai kimanin 30,000[9], ya nuna irin ƙoƙarinsu ga aikine ya sa suka ƙwato uwar gidan kakakin majalisar dokokin jihar Osun, ga kuma irin rawar da kungiyar ta taka wajen yaƙi da Boko Haram.

Wannan yayi daidai da kirarin da Dan taragon Fatara yayi cikin kirarinsa har yake cewa "A ba su dama su shigo yaƙi da 'yan fashi da sauran 'yan ta'adda a Nijeriya. Wannan muƙala ta ga buƙatar hukumomi su dubi batutuwa irin na Ɗan taragon Fatara ga makomar ƙasashe ba wai Nijeriya da Nijar kawai ba, har ma da sauran duk ƙasashen Afirka baki ɗaya, musamman idan an dubi yadda matsalar rashin tsaro ta yi katutu, a yau ga Sojoji da sauran jami'an tsaro da makamai a yankunan Afirka amma tsaro da kwanciyar hankali sun faskara a tsakanin al'ummomin wannan yanki. Shawara a nan ita ce, duk ƙasar Afirka da ke da 'yan tauri to ta yi tunanin haɗa su da jami'an tsaronta wajen yaki da ta'addanci ta gwada ta gani kamar Nijeriya ta haɗa haɗakar 'yan banga da jami'an tsaro (Civilian Joint Task Force).

[9]Freedom Online

## Manazarta


Bargery, G.P (1934) *A Hausa EnglishDictionary & Hausa Vocabulary,* LondonOxfordUniversity Press.

Birniwa, H.A (2004) *Siffantawa a cikin waƙoƙin Siyasa Ɗunɗaye Journal of Hausa studies vol. 1 No. 1* Department of Nigerian Languages, U.D.U.S Sokoto.

Bunza, A.M. (1990) "Hayaƙi fid da na kogo" (Nazarin Siddabarun Hausawa) Kundin Digiri na Biyu Jami'ar Bayero Kano.

Bunza A.M. (1995) "Magani A Rubuce"Kundin Digiri na uku, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero Kano.

Bunza, A.M. (2015) "Zaman lafiya da tsaro a Daular Musulunci ta Sakkwato: (Abin koyi ga shugabannin Zamaninmu". Takardar da aka gabatar a taron yini ɗaya da Centre for Interllectual Services in Sokoto Caliphate ta shirya na faɗakarwa a kan muhimmancin tsaro da zaman lafiya a Karƙashin koyarwar Shugabancin Daular Musulunci ta Sakkwato 31 ga Janairu, 2015.

Commolli.V.(2015) *Boko Haram: Nigeria' Islamists Insurgency,* London, Hurts and Company.

Ɗangambo, A.(1984)*Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*, Kano,Triump.

Ɗangambo,A.(2007) Ɗawayar Gadon Feɗe Waƙa, Kaduna, Baraka Press and Publication Limited.

Gusau, S.M (2009):*Diwanin Waƙoƙin Baka:* Zaɓaɓɓun Mantanoni na waƙar Baka na Hausa, Kano, Century Research and Publishing Company Limited.

Gwarzo, M. (1934):*Idon Matambayi;* Zaria , N.N. P.C.

Ibrahimm M.S.(1983):*Kowa Ya Sha Kiɗa*, Ibadan, Longman Nigeria.

Imam, A. (1937):*Magana Jari Ce 1;*Zaria , N.N. P.C.

Jami'ar Bayero (2006):*Kamusun Hausa*; Zaria, Ahmadu Bello University Press,

Junaidu I. da 'Yar'aduwa, T.N.(2007): *Harshe da Adabin Hausa Kammalalle Don Manyan Makarantun Sakandare*; Zaria, Spectrum Books Limited.

Okeke V.O.S.(2013:"Community Policing, Vigilante Security Apparatus and Security Challenge in Nigeria; A lesson from Britain and Igbo traditional Security in Nigeriya" British Journal of Arts and Science

Kamuaun Hausa (2006) *Wallafar Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya,* Jami'ar Bayero Kano.

Sayaya, A.S. (2009): *Wasannin Tauri A Waƙar Katsina, Kundin kammala Digiri na Biyu* Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato.

Tafawa Ɓalewa, A. (1934) : *Shaihu Umar*, Zaria, N.N.P.C

Skinner, N. (1980): *An Anthology of Hausa Literature*,Zaria, NNPC.

Smith, M. (2015): *Boko Haram Inside Nigeria's unholy war*, I.B. London, Tauris & Co. Limited.

Umar, M. B. (1987): *Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya,* Kadun,Triumph.

Yahya A.B. (1997) :*Jigon Nazarin Waƙa*, FISBAS,Kadun Media Service.

Yahya, A.B. (1999):*Salo Asirin Waƙa*, FISBAS,Kadun Media Service.